# Gabatar da Sirri

Mahalarta taron za su bincika sirrinsu da kansu da kuma tasirin da yake da shi a tasu rayuwar. Mahalarta taron za su yi la’aƙari da nau’in bayanin da suke so su adana cikin sirri da kuma rubutun da za su yi / ba za a raba wani ƙayyadadden bayani ba.

## Kayayyaki darasi

Takardar Darasi a kan Wasan Sirri

# Me “Sirri” Ke Nufi a Gare Ka?

## Wasan Sirri

### Tattaunawa a Aji

Raba Takardun Wasan Sirri

### Sanar da Ɗalibanka

Kai ne ke yanke hukunci game da sirrinka a kowace rana, musamman a lokacin da ka kasance a kan intanet sannan kuma kake yin amfani da wayarka ko wasu na’urori masu aiki da lambobi. Sau da yawa, wata ƙila ba za ka ɓata lokaci da yawa ba wajen yin tunani game da kowane ɗaya daga cikin waɗannan hukuncin. Amma sun ƙara duka domin su zama taka fahimtar sirrin ta musamman.

Sirri wata dama ce ta kula da abun da wasu mutanen suka sani game da kai. Za ka iya yin wannan ta hanyar faɗin wasu abubuwan game da kanka (kamar sanar da wasu mutanen adireshinka ko abun da kake son yi don nishaɗi) ko yin abubuwa a kewaye da wasu mutanen (kamar zuwa kanti tare da abokanka da kuma ɗaukar abun da ka fi so). Sirrin na da tasiri ko kana cikin ɗaki tare da wasu mutanen ko kuma kana yin magana da su ta intanet.

An gina sirri ne bisa ga naka hukuncin da ka yanke. Abun da sirri ke nufi a gare ka da iyalinka zai iya bambanta a kan abun da sirri ke nufi ga wasu mutanen a cikin wannan ƙungiyar da iyalansu. Idan muna da masaniya a kan abun da muke darajawa a matsayin sirri, da kuma yanda ɗabi’unmu a kan layi za su iya tsara sirrinmu, za mu iya yin zaɓin da ya dace game da wane irin nau’in sirri muke so.

Yanzu za ka kasance a cikin wani wasa mai sauri game da sirri [ka ɗan tuntuɓi Takardar Darasin Wasan Sirrin] da za su taimaka maka wajen duba abun da kake tunani ko ji game da sirri. Za ka cike takardun darasinka kowannen ku, zagaye ɗakin da shi, sannan ka gabatar da kanka ga wani mai halartar taron. Kai da wani halartarcin taron za ku yi wa juna tambayoyi game da bayanan da ke cikin takardar darasin. Karka nuna takardar darasin ga wasu musu sauauen! Ba za a karɓi takardar darasinka ba a ƙarshen ayyukan — kana da ‘yancin kai shi gida ko ka jafar da shi idan kana so

A cikin kowace fira, dole ne kowane mahalarcin taron ya raba a ƙalla amsoshi guda uku ga tambayoyin da wasu mahalarta taron suka yi. Mahalarta taron za su iya zaɓar su raba sama da guda uku. Mahalarta taron su ma za su iya zaɓar wasu guda uku ne ko kuma ƙarin bayanai za su raba. Bayanai guda nawa ne kowane mahalarcin taron zai raba? Wane bayani ne kowane mahalarcin taron zai raba? Bari mu tafi sannan mu tattauna!

### Tattaunawa a Aji

Mahalarta taron sun cike takardun darasin. Sannan ka ba mahalarta taron mintuna 15 don su kewaye ɗakin sannan su yi magana da juna. Bayan nan, kasance cikin tattaunawar tare da ƙungiyar gaba ɗaya ta hanyar yin amfani da waɗannan tambayoyin. A ƙarshe, ka tabbata mahalarta taron sun yi wurgi da takardun darasinsu ko su kasance tare da su — a matsayin masu ilmantarwa, kar ka karɓi takardun.

## Tattaunawa

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin akwai wasu hujjojin da ba ka raba da wani ba? Waɗanne? Me yasa?

Wasu hujjojin ka raba? Me yasa?

Shin kowa da kowa ya yanke hukunci iri ɗaya game da abun da za ka raba? Me yasa / me zai hana?

Ya danganci wanda za ka raba da shi, me zai sa ka raba da yawa, ko kaɗan, na irin wannan bayanin? Yaushe za ka raba shi?

Shin akwai wani abun da ka raba a lokacin wannan aiki da ba za ka raba shi da duk wanda ka sani ba? Me zai hana?

Shin irin wannan bayanin na kowa da kowa ne? Na sirri ne? Me yasa? Shin wannan iri ɗaya ne ga kowa da kowa?

**Sanar da Ɗalibanka**

Kamar yanda ka ji yanzun nan, mutane na yanke hukunci mabambanta game da abun da za su raba da kuma abun da ba za su raba ba. Haka kuma suna da dalilai da yawa ga zaɓinsu.

Abun da muka yi yanzunnan wasa ne. Amma muna yanke waɗannan hukuncin iri ɗaya a kowace rana a rayuwa ta zahiri. Muna yanke hukunci ko za a yi aike da wasu hotunan da aka ƙayyade a dandalin sadarwar zamani. Muna yanke hukunci ko muna so ko kuma ba ma son wasu ƙayyadaddun bayanan tuntuɓa, kamar adireshin imel ɗinmu, wanda kowa da kowa zai iya ganinsu a kan asusun dandalin sadarwar zamaninmu. Abun da muka yanke hukunci a kai zai iya bambanta da abun da aminanmu suka yanke hukunci a kai ko kuma ma abun da muka yanke hukunci a kai a watan da ya gabata. Ko da kuwa mun yanke hukunci iri ɗayi a lokuta mabambanta, dalilanmu za su iya bambanta.

Waɗannan hukunci da dalilan za su wakilci fahimtarmu ta ƙashin kanmu a kan sirri.

An bayyana cikin sauƙi, sirri yana nufin yanda muka zaɓa mu kula da bayanai game da kanmu. Wannan bayanin zai iya haɗawa da wasu ɓangarori na bayyana kanmu,

ayyuka, abubuwan da aka fi so, al’amuran yau da kullum, da sauran ɓangarorin rayuwarmu. A wannan duniyar da muke ciki yau, akwai wasu damarmaki da yawa fiye da na da domin raba bayanai game da kanmu tare da wasu. Saboda haka yana muhimmanci mu zama muna da masaniya a kan tamu fahimtar a kan sirri, kuma wannan yasa muka yi tunani game da ko mun gamsu da fahimtar ko kuma a’a.

**Tambayi Ɗalibanka**

Bisa ga ɗabi’unka dangane da wasa game da sirri, da kuma ɗabi’unka a rayuwar yau da kullum, yaya ka bayyana sirri? Me yasa?

Shin duk bayanan sirri su ma sirri ne?

1. Ba dole ba ne. Misali, ranar haihuwarka ba za ta iya kasance sirri ba kamar yanda abubuwan da aka shigar a dayarinka suke. Akwai mutane da yawa a duniya waɗanda suka san ranar haihuwarka da kuma waɗanda suke buƙatar su sani, kamar iyayenka / masu kula da lafiya ko likitanka. Amma saboda wani abun ba sirrin ba ne, duk da haka za ka iya ɗaukar shi a matsayin sirri. Mafiya yawa daga cikinmu ba ma son kowa da kowa ya san ranar haihuwarmu saboda muna ganin waccan a matsayin bayanin da mutanen da ke kusa da mu ne kawai ko kuma mutanen da ke da wani dalili na musamman ne kawai ya kamata su samu. Irin waɗannan hukuncin da aka yanke game da wanda ya kamata ya san wani abu game da mu, yaushe, kuma mene ne dalilin makullin sirrin.

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin akwai wasu abubuwan da ba su zama wajibi su zama sirri ba da kake so ka sirrinta su daga wurin mutanen da ba ka sani sosai ba / mutanen da ka haɗu da su yanzu?

1. Lambar waya, imel, hotuna, bidiyoyi, da dai sauransu

Shin akwai wasu abubuwan da ka ɓoye wa iyayenka / masu kula da lafiya ko kuma abokanka? Yaya malamanka ko sauran masu ilimantarwar?

1. Sakamakonka a makaranta, asusun Instagram ɗinka, dayari ɗinka.

Shin ka koyi wani abu game da fahimtar sirri ta ƙashin kanka da ta ba ka mamaki?

**Sanar da Ɗalibanka**

Za ka iya kasancewa tare da Wasan Sirrin bayan mun gama yau! Yanzu da kake ƙara yin tunani game da sirri, za ka ga damarmakin da ba su ƙirguwa don yin zaɓi a kowace rana na inda za ka sanya taka fahimtar ta sirri a aikace.

# Aiki

## Aiki

### Sanar da Ɗalibanka

Yanzu za mu ƙara bincika yanda ka fahimci sirrinka.

1. Nemo wasu misalai guda uku a intanet inda wani ya raba wani abu ko kuma ya aike da wani abun da za ka adana cikin sirri da kanka. Waɗannan za su iya zama daga wurin wani ɗan wasa, ɗan siyasa, ko shugaban kasuwanci, ko kuma za ka iya bincikawa ta hanyar yin amfani da alamar hash ko bincike gaba ɗaya a intanet don gano misalai barkatai. Gwada nemo nau'o'in abubuwa (misali., hotuna, bidiyoyi, aike mai ɗauke da rubutu, kamar jawabin da wani ya yi a dandalin sadarwar zaman da / ko a kafar watsa labarai) a kan batutuwa daban-daban.

2. Ga kowane misali, tsara sakin layi guda ɗaya kana mai yin bayani a kan dalilin da yasa ka zaɓi ka adana wannan bayanin cikin sirri. A cikin sakin layinka, ka ɗan yi bayanin in / yanda ra'ayinka ya canza a kan raba wannan bayanin wanda ya danganci rubutun (misali., wanda kake hulɗa da shi, yawan mutanen da ke cikin tattaunawar, dalili da manufa, muhalli [makaranta da wajen makaranta]).

### Aiki

Ba mahalarta taron mintuna 40 domin su kammala aikin.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.